# Dokokin Majalisar Dunkin Duniya a cikin tafin hannunka



United Nations

## Saƙo daga babban sakatare

A cikin rabin ƙarnin da ya wuce, kundin dokokin majalisar ɗunkin duniya ya kasance tarsashin gina dangantaka a tsakanin ƙasashe. Duk da canji mai yawa da aka samu bai sanya ra'ayin haɗin kan duniya da kun din ke ɗauke da shi ba ya rasa Ivin ingancin da ya ke da shi ba. A yau, kundin ya kasance babban sinadarin haɗan kan duniya domin samun zannan lafiya da cigaba.

Yayin da dokar ke bayanin ƙa'idojin duniya da fatarsu, ta samar da sauƙi wajen zarfar da dokokin. Hangen nesan marubuta dokar-domin tsirar da ƙasashe masu tasowa daga bala'in yaƙi, ƙarfafa imani da haƙƙoƙin Bil'adama, shata sharuɗɗan kaiwa ga samun mulkin demokuraɗiyya, har-ila-yau don bunƙasa kin daɗin jama'a da kanfafa ingantacciyar rayuwa mai ƙunshe da 'yanci ga kowa-wannan dole ne a karfafa shi duk halin da aka sami lokaci.

A yau hanyoyin rayuwar gargajiya na nan na baiwa sabuwar ingantacciyar rayuwa ta zamani a duniya wuri. Domin mu na ganin ƙaidogin kan duniya suna da dangantaka ta ƙud-da-ƙud da juna, don haka dole ne a yi gwagwarmayar hakan bai ɗaya. Cikakken ƙudurin ciyar da al'uma gaba alsu ne muhimmi idan waɗannan aloubuwan da ile jawo sabani ana son a kawar da su baki ɗaya. Kunna saɓani (yaki) da ya dabaibaye duniya a yau dole ne a walwale shi; a waman lokacin ne kwai ciyaga– da ya ke shi ne manufarmu zai sami tabbata.

Kundin dokokin wani cigaba ne na Bil'adama. Wasu takardun tarihi ne mai fuskoki iri-iri, kuma wata dukiya ce ta alfarima ga mutum. Dun haka samun sa wani abin yin buki ne da annashuwa.

Dun haka bukin cikon shekaru hamsin lokaci ne na tunawa da abin da ya gabata da sabunta niya. Yayin da mutanen cikin ƙungiyar majalisar ɗunkin duniya ke cikin ruɗamin abin da zai zo a gaba, kundin dokokin majalisar ɗunkin duniya abu ne da zai zamo ja-makafi domin ciyar da mutane gaba. Dun haka dole ne a sake yin Kudurin ciyar da ra'ayin kundin gaba. Dole ne a sami sabon karfi da juriya domin fuskantar duk wata barazana da zata taso nan gaba. Ingantattun hanyoyin juriya da kundin ya ƙunsa yana gayyatar duk al'uma mai tasowa ga ta sabunta alƙawarin ganin haɗin kan al'uma.

Buturus-Buturus-Ghali
Babban sakataren majalisar dunkin Ɗuniya

# Dokokin Majalisar Dunkin
# Duniya a cikin tafin hannunka



A Translation of the "United Nations Charter at your finger tips" Into Hausa

Mukaddima: Mu jama'ar Majalisar Ɗunkin Duniya

| | |
|---|---|
| Babi 1 | Dalilai da ƙa'idoji |
| Babi II | Ɗan ƙungiyar (mamba) |
| Babi III: | Rassa |
| Babi IV: | Babban taro |
| Babi V | Majalisar tsaro |
| Babi VI: | Sashen sulhunta saɓani |
| Babi VII: | Matakan da ake ɗauka kan barazana ga zaman lumana, karya zaman lafiya, da shisshigi ga wata ƙasa |
| Babi VIII: | Tsarin Nahiyoyi |
| Babi IX: | Kungiyar tattalin aziki da jin daɗin jama'a ta duniya |
| Babi X: | Kuduri akan ƙasashen da basu da mulkin kai |
| Babi XII: | Tsarin amintattu na Duniya |
| Babi XIII: | Kungiyar amintattu |
| Babi XIV: | Kotun Duniya |
| Babi XV: | Sakatariya |
| Babi XVI: | Kanan tanadi |
| Babi XVII: | Tsarin tsaron wuccin gadi |
| Babi XVIII: | Gyare-Gyare |
| Babi XIX: | Amincewa da sa-hannu |

## 1 Mene ne kundin dokoki?

Kundin dokoki dai wani tsarin mulki ne da ke ɗauke da dalil ai da manufofin kafa majalisar Ɗunkin Ɗuniya. Kuma wani irin sulhu ne da ƙasa take sanya wa hannu ta amince zata bi kumata mutunta lokacin da ta yarda ta zano mmbar wannan ƙungiyar. Kundin dokokin yana ƙunshe da babi 19 da suke ɗauke da kokoki III. Shi kundin ainihin an ajiye shi ne a ɗakin ajiyar littattafan ƙungiyar majalisar ɗunkin duniya ne.

Matsayin kotun duniya duk da ya ke wani sulhu ne na daban, amma duk da haka wani yanki ne na kundin dokokin. Duk ƙasar da ta zamo mambar majalisar Ɗankin Ɗuniya to nan take ta amince da matsayin katun duniya ke nan.

## 2 Yau she he aka tsara kundin dokokin?

An fara tsara kundin ya zuwa kammaluwar sa ce domin a rattaba masa hannu a 1945. A cikin watan Afirilu 1945 ƙasashe 50 suka hadu a birnin san Francisco domin tattaunawa ta ƙarshe da zata haifar da ƙungiyar majalisar Ɗunkin Duniya. Bayan daguwar tattaunawa sai aka buɗe kundin dokokin domin ƙasashe su sanya masa hannu a cikin watan Yuni 1945, Ya zama cikakkiyar doka da aka fara aiki da ita a 24 ga watan oktoba 1945. Tun wannan lokacin ne akan yi bikin tunawa da ranar da majalisar Ɗunkin Ɗuniya ta kafu a 24 ga oktoba duk shekara.

## 3 Mene ne babban dalilan da tsarin kundin dokoki ya da na kafa majalisar Ɗunkin Ɗuniya?

Muhimmau kafa ƙungigar sune:

- Tabbatar da zaman lumana da tsaro a tsakanin ƙasa da ƙasa;
- Bunƙasa kyakkyawar alaƙa tsakanin ƙasashe.
- Haɗa kai domin a yi aikin ɗaukaka hanyoyin rayuwar jama'a, da bunkasa mutunta haƙƙoƙi da 'yancin Bil'Adama; da
- Kasancewa cibiyar taimakawa ƙasashe su kai ga waɗannan bukatu.

## 4 Mene ne kundin dokar ya ce dangane ƙasa mai mulkin kan ta?

Dokta ta 2 a cikin kundin dokokin ta ce majalisar Ɗunkin Ɗuniya ta ɗauki duk ƙasashen da ke cikin ta daya ne, babu wata da tafi wata. Ba wai wata gwamnatin mulkin duniya ba ce, sai dai tana samar da hanyoyin walwale matsaloli da duk wani abin da ke ciwa Bil'adama tuwo a ƙwarya. Babu wani tanajin doka a cikin kundin da ya baiwa majalisar Dunkin Duniya damar yin katsalandan a cikin harkokin cikin gidan wata ƙasa. Haka ba'a bukaci wata ƙasa ta kawo harkokin cikin gidanta ba a gaban majalisar Dunkin Duniya domin ta walwale mata shi ba.

Ana bin fassarar halshen da aka yi amfani da shi a cikin kundin da sauna !dan ya shafi harkokin cikin gidan wata ƙasa. Amma duk wata matsalar da majalisar tsaro ke ganin na iya zama barazana ga tsaro da zaman lumana ana iya tattauna ta. Har-ila-yau duk wani keta haƙƙin Bil'adama da wata kasa ke yi sashen da ya dace na majalisar Ɗunkin Ɗuniya na da daman ya tattauna shi.

## 5 Mene ne muhimman rassan majalisar Ɗunkin Duniya da kundin dokar ya ƙirƙiro?

Majalisar Ɗunki Ɗuniya na da rassa Muhimmai guda shida. Sune Babban taron majalisar, majalisar tsaro, majalisar tattalin arziki da jin daɗin jama'a, majalisar amintattu, kotun duniya, da sakatariya. Duk mazauninsu na nan a hedikwatar majalisar Ɗunkin Ɗuniya da ke New York, ban da na kotun duniya da mazauninta ya ke a Hague, ƙasar Netherlands.

| | | |
|---|---|---|
| Kotun duniya | Babban taron | Majalisar tattalin arziki da jin daɗin majalisa jama'a |
| Majalisar tsaro | sakatariya | majalisar amintattu |

## 6 Wane reshe ne ya ƙunshi duk ƙasasheen da ke cikin majalisar Ɗunkin Ɗuniya, kuma mene ne irin aikinsa?

Babi na IV na magana ne akan Babban taron majalisar Ɗunkin Ɗuniya, wanda ke da matsayin mai kula da aikace-aikacen duk sauran rassan majalisar Ɗunkin Ɗuniya. Alƙalami na 9 ya bayyana cewa Babban taron Majalisar Ɗunkin Ɗuniya ya ƙunshi duk ƙasashen da ke cikin ƙungiyar majalisar Ɗunbin Ɗuniya ne. Babban taron na iya tattaunawa akan duk matsalar da ta shafi zaman lumana a duniya, kuma ya ba da shawarwarin da suka dace, amma ban da matsalolin da dama can majalisar tsaro ta riga ta tattauna akan su dai-dai da irin tanadin da kundin doka ya amince da shi. Babban taron na karɓar rahoto dada sauran rassan majalisar Ɗunkin Ɗuniya da kuma Babban sakataren majalisar. Da amin... war majalisar tsaro ne Babban taron ke karɓar sabin mambob... cikin majalisar Ɗunkin Ɗuniya, haka da amincewar sune ake naɗa wa majalisar sabon Babban sakartare (magatarkarda). Duk shekara ce ake zaben sabin mambobin majalisar tsaro guda biyar da basu da kujerin dindindin. Babban taron ne ke da alhakin yanke irin kason da kowace ƙasa zata baiwa majalisar Ɗunkin Ɗuniya da kuma yadda za'a kashe kuɗin majalisar—sai mu ce wannan majalisar ce wuƙa da nama.

Babban taron majalisar Ɗunkin Ɗuniya na iya ɗaukan matakai akan duk wan... 'amari da ya shafi majalisar Ɗunkin Ɗuniya kamar haƙƙin Bil'adama, yawan jama'a, sha'anin raya ƙasa, ƙayyade makamai, Muhalli, Miyagun ƙwayoyi, 'yan gudun hijira, dokokin da suka shafi ruwa (teku) ko sararin samaniya kaɗan ke nan daga cikinsu. Yana bunƙasa haɗin kai, kuma ya shata hanhoyin hulɗar difilomasiyya tsakanin gwaunatoci.

Yawancin hukunce-hukuncen Babban taron majalisar bai zamo tilas ga ƙasashe ba, sai dai yana akan matsayin shawarwari ne gare su, watau za'a name su da su ɗauki matakan da suka dace akan matsalolin. Har-ila-yau hukuncin

Babban taron yana matsayin hukuncin da al'umar duniya suka yanke ne. Babban taron majalisar na yanke hukunci akan wasu nau'o'in sulhu-sulhu, kuma idan har aka sami wani kashi na mambobin majalisar suka amince da shi ya zama doka ke nan da ƙasa-shen duniya zasu yi amfani da ita.

## 7 Wane reshe ne ke da haƙƙin tabbatar da zaman lumana da tsaro, kuma mambabi nawa ne ya ke da shi?

Kundin doka aya ta V ta ce majalisar tsaro shi ne reshen majalisar Ɗunkin Ɗuniya da ke da haƙƙin tabbatar da cigaban zaman lumana da tsaro a duniya. Duk ƙasashen da ke cikin majalisar Ɗunkin Ɗuniya sun yi alkawarin yarda da kuma zartar da hukuncin da majalisar tsaro ta yanke.

Majalisar tsaro zata yi ƙoƙarin sulhunta saɓanin da ke tsakanin ƙasashe, ta hanyar shirya tattaunawa, ko aika tawaga ta bincika, ko aika sojoji domin shiga tsakani. Kuma majalisar na ba da shawarar sabin mambobin da zasu shiga majalisar Ɗunkin Ɗuniya ga Babban taron majalisar, da kuma wanda ya dace a zaɓa ya zama Babban magatakardar majalisar Ɗunkin Ɗuniya, kai zasu yi zaman hadin gwiwa tare da Babban taron majalisa domin zaɓen mambobin da zasu yi aiki a kotun Ɗuniya.

Majalisar tsaro na da mambobi 15. ƙasashe biyar daga cikinsu na da kujerar dindindin sune-sin, Faransa, RAsha, Burtaniya da ƙasar Amerika; sune manyan sojojin tarayya lokacin da aka yi yaƙin duniya na 11. Akan kuma zaɓi ƙasashe goma daga duk nahiyoyin duniya da zasu zama 'yan majalisar tsaron da basu da ikon hawan kujerar na ƙi (duba a tamboya ta 21).

## 8 Mene ne kujerar na ƙi kuma a ina ne aka ambáce shi cikin kundin doka?

Kujerar na ƙi na da alaka ce kawai da majalisar tsaro, Ana iya tsayar da magana muhimmiya idan ɗaya daga cikin Mambobin majalisar tsaro ya jefa ƙuri'ar ƙin yarda, amma babu wurin da kundin dokoki ya ambaci kalmar na ƙi (veto) sai dai wanka da kaman jirwaye da Ayar doka ta 27 da ta yi, wanda ya nemi sai duk mambobin dindindin na majalisar tsaro sun jefa ƙuri'ar yarda baki ɗaya, shi kun ga an fassara shi da nufin yarda, ko ƙin yarda ko ƙin jefa ƙuri'ar ma baki ɗaya ga wata ƙasa mai kujerar na ƙi. Domin haka ne aka ce ƙasashe biyar masu kujerar na ƙi na da wani ƙarfi na musamman.

## 9 Wane babi ne ya yi magana akan yadda za'a tabbatar da zaman lumana ko dawowa da shi?

Babi na VI ya yi magana ne akan hanyar sulhunta saɓani a cikin ruwan sanyi, wanda ya haɗa da matakai irin su tattaunawa, aika masu sa idanu ko kaiwa a kotu. Majalisar na iyau murtar ƙasashen su tattauna a tsakanin su ko su shata yadda za'a yi sulhun. Sauran hanyoyin da aka cika amfani da su sun haɗa da aika masu bincike ko tawagar gano gaskiyar lamarin, ko su nemi Babban magatakardar majalisar Dunkin Duniya ya yi amfani da "Ofishinsa" domin samar da zaman lumanar.

Babi na VII ya yi magana ne akan yin amfani da ƙarfi da wasu matakai. Wanda ya ƙunshi irin matakan da za'a ɗauka ne idan shisshigi ya cigaba, idan akwai barazana ga zaman lafiya kuma waɗanda abin ya shafa basu mutunta hukuncin da majalisar tsaro ta yanke ba. Majalisar tsaro na iya ɗaukan wasu matakai tsaurare kamar. Banye takunkumin sayen makamai ko takunkumi a fannnin tattalin arziki, sannan su kuma sauran ƙasashe su yanke hulɗan jakadanci da su, ko ɗaukan matakan soja. A cikin watan Agusta 1995, akwai takunkumin difilomasiyya, da na tattalin arziki mai tsauri ko sauƙaƙƙe a kan ƙasashe bakwai da ke cikin majalisar ɗunkin duniya sunce ƙasar-Angola, Iraq, Laberia libya, somalia, da tsohuwar ƙasar Yugoslabiyar haka a watan Agusta 1995 majalisar tsaro ta wanke gwaunatin Rwanda daga takunkumin sayen makamai da aka sanya mata a shekarar 1994 amma dokar ta cigaba da amfani kan sojojin sa-kai .

Yan shekaran nan majalisar tsaro ta yi kira ga a ɗauki wasu matakai da ba'a yi bayanin su ba a cikin kundin doka amma ya shiga cikin fassarar da aka baiwa ɗaukar matakai. Misali, majalisar tsaro a 1991 ta kafa wata tawagar da zata lura da kwance harkokin saje akan iyakar iraq-kuwait.

Bayan haka ne a watan mayju 1993 majalisar ta tabbatar da cewa shawarar da wannan tawagar ta yanke ta shata iyaka tsakanin ƙasar iraq da kuwait ya yi kuma babu sake.

Har-il-yau, majalisar ta yanke shawarar kafa wata kotu a watan mayu 1993 da zata tuhumci mutanen da aka zarga da keta alfarmar 'yancin Bil'adama a tsohuwar kasar Yugoslabiya, da kuma wata kotun a ƙasar Rwanda a watan Nuwamba 1994. Duk waɗannan shawarwarin an yanke sune a ƙarƙashin Babi na VII a kundin dokokin.

Har-ila-yau abin lura ne cewa alkalami na 51 na kundin kokokin ya yi tanadin cewa, idan aka kaiwa wata ƙasa farmaki zata iya ɗaukan matakan kariya ita ɗaya ko da haɗin gwiwar wasu ƙasashen kafin majalisar tsaro ta ɗauki matakan da zai maido da zaman lumana a wajen.

## 10 Wane sashe ne na kundin dokar da ya shafi tabbatar da zaman lumana dahar yanzu ba'a fara aiki da shi ba?

Kundin dokar an gina shi da aƙidar samar da tsaro ga taro, abin nufi shi ne ta'addanci ga wata ƙasa tamkar ta'addanci ne ga duk ƙasashe baki ɗaya. Kuma ana iya cewa yaƙi a wani wuri haɗari ne a ko'ina. Tabbas ne cewa idan ƙasashen duniya suka yi taron dangi ga ƙasa zata hanu daga tayar da tashin hankali a duniya.

Kasashe zasu yi wa majalisar tsaro tarbacen sojoji, kuɗi da kayan aiki domin tabbatar da zaman lafiya da tsaro. Wa ɗana sojojin da aka "kira" zasu zauna a ƙarƙashin hafsan kwamitin sojojin da ke wakiltar shunwagabannin sojojin ƙasashen da ke da kujerun dindindin a majalisar tsaro.

Aikin kwamitin shi ne taimakawa majalisar tsaro da shawarwari da duk irin abin da soje ke bukata domin tabbatar da samun lumana da tsaro a duniya, har-ila-yau, ƙayyade makamai da kwance ɗamara duk aikin wannan kwamitin ne. Duk da haka dai da aka fara yaƙin cacar baki bayan an kafa majalisar Ɗunkin Ɗuniya, ba'a yi amfani da waɗannan shawarwari ba; Don haka alƙalumman doka ta 43 zuwa 47 ba'a taba aiki da su ba.

## 11 Wasu Babi ne na kundin dokokin ya yi magana akan kawo zaman lafiya?

Shi dai sojan kawo zaman lafiya babu inda aka ambace shi a cikin tsarin mulkin majalisar ɗunkin duniya. Wata dabara ce dai da majalisar ɗunkin duniya ta ɓullo da ita domin magance yaƙi, shi dai kawo zaman lafiya ya ƙunshi yin amfani da sojojin ƙasashe daban-daban ne a ƙarƙashin jagorancin majalisar ɗunkin duniya domin shiga tsakanin ƙasashe ko sojojin da ke yaƙar juna kafin a samar da kwanciyar hankali irin ta siyasa. Duk irin kawo zaman lafiyar da majalisar ɗunkin duniya ta shiga a tarihinsa ya kasance sassauƙa ne kuma kai tsaye yake. Kasashen da ke cikin majalisar ɗunkin duniya zasu yi tarbacen sojoji a ƙarƙashin jagorancin Babban sakataren majalisar ɗunkin duniya. Duk sassan da ke saɓanin sukan yi murna da zuwan sojojin shiga tsakanin, da za'a rarraba domin kula da tsakaita yaƙi ko wata yarjejeniya da aka ƙulla.

Kawo zaman lafiya a yau ya zama lamari mai tsanai, domin yawa da munanan salon da yaƙe-yaƙe ke da shi a yanzu. Yaƙe-yaƙen da ake fama da shi na basasa ya fi yawan yaƙin da ake yi tsakanin ƙasa da ƙasa, a aikace-aikacen kawo zaman lafiyan 'yan shekarun nan an aika da masu kawo zaman lafiya zuwa wuraren da ba wasu alkawulla; inda ke yawan tuntuɓar majalisar ɗunkin duniya; da inda babu gwamnati ko kuma inda sha'anin siyasa ya taɓarɓare. Kawo zaman lumana ba wai kawai na nufin shiga tsakanin ƙungiyoyin da ke yaƙi ba a wannan sabon ƙarnin, a'aya ɗauki sabon salo da ya ha ɗa da bincikawa ko ana bin alkawurran da aka ƙulla, lura da zabe, bunƙasa mutunta haƙƙin Bil'adama, kwance ɗamarar ƙungiyoyin da ke yakar juna; sa idanu da horon 'yan sandan ƙasashe, kare yawan farar hula da tabbatar da cewa tawagar da ke kai kayan agaji ta sami nasarar yin hakan.

Rahoton da Babban megatakardar majalisar ɗunkin duniya ya shirya a cikin shekara 1992 mai taken "matakan kawo

zaman lafiya" ya shata shawarwari da dama da zasu faɗaɗa kuma su ƙarfafa kawo zaman lafiyar ƙungiyar ɗunkin duniya, musamman domin samun isasshen ƙarfin tattalin arzika da irin sabon salon da aikin ya samu. Misali ya kira ga a samar da asusun aika sojojin kawo zaman lafiya, domin a yi amfani da shi wajen fara wani sabon aikin kawo zaman lafiyar da ya samu. Babban taron majalisar ɗunkin duniya ya kafa wannan asusun a watan Disambar 1992 da fatar za'a sami dala Miliyan 150 ($150 million) amman har yanzu ba'a cimma wannan adadin ba. Gwamnatoci ma an neman su da su taimaka ga wannan asusun ta hanyar ɗaukan sojojin kyauta da taimaka masu a hanyoyin dabarun yaƙi. Har-ila-yau za'a taimaka wajen horar da masu kawo zaman lafiyar, sojoji da farar hula. Dabarun tsare-tsare da shugabantar sojojin abu ne da za'a ƙarfafa.

A cikin "Matakan kawo zaman lafiya" Babban magatakardar majalisar ya bayar da shawarar cewa a kafa wata runduna ƙarama da zata ƙunshi 'yan ƙasashe daban-daban mai issahen horo a ƙarkashin mamalisar tsaro da za'a iya kai da sauri a wuraren da ake tarzoma (yaƙi). Amma wannan ra'ayi na Babban Sakataren har yanzu majalisar tsaro ba ta amince da shi ba.

Wata shawarar da "matakan kawo zaman lafiyar" ta bayar shi ne samar da wata rundunar ko-ta-kwana domin kawo zaman lafiya, wadda ana nan yanzu ana yin ƙoƙarin yin hakan. A cikin watan Agusta 1995 wasu ƙasashe 47 sun ba da sajojinsu na ko-ta kwana da suka kai 65,000. Wannan tsarin na ko-ta-kwana zai baiwa majalisar ɗunkin duniya damar kai sojojin kawo zaman lafiya duka inda ake bukatarsu.

A cikin "Karin matakan kawo zaman lafiya" da ya fito a watan janairu 1995, Babban magatakardar majalisar ya nunar da cewa duk yake-yaken da ake fama da su a yau na cikin gida ne, masu yin wannan yaƙin kuma sune sojoji da kuma sojojin sa-kai, don haka farar hula ce suka fi shan wuya kuma wannan yaƙin na rusar da al'adu. Yaƙe-yaƙen

"zamani" da ake fama da su sun fi shafar abubuwan jin ƙai da shuwagabannin ƙasa basu da ikon magancewa.

Babban magatakardar majalisar ya ce yawancin ra'ayin da ke cikin "matakan kawo zaman kafiya" sun nuna masu ingance ne don haka matakan kawo zaman lafiya da na tabbatar da zaman lafiyar dole ne a cigaba da inganta su. haka a cikin Karin matakan kawo zaman lafiya" shima ya yi bayanin sassan da ya kamata kasashe su ɗauki matakai masu tsauri. Sun kuwa haɗa da sha'anin kuɗi, bayyana wa sojojin kawo zaman lafiya aikinsu, da kuma aikin kawo zaman lafiyar da aka aiwatar tare da haɗin gwiwan ƙungiyoyin nahiyoyi.

12

**Mene ne kundin dokokin ya ambata a kan shirin da Nahiyoyi suka yi?**

Tsarin mulkin ya sadaukar da Babi na VII ne akan shirin da ƙungiyoin nahiyoyi ke yi ko kafafensu. Ana bukatar ƙasashe su yi ƙoƙarin walwale matsalolin nahiyoyinsu a ƙarƙashin ƙungiyoyin Nahiyoyin kafin su kawo su gaban majalisar tsaro. Kafafen Nahiyoyi na iya ɗaukan matakan amfani da soje tare da izinin majalisar tsaro.

Tsarin mulkin bai ba da takamammen surar waɗannan ƙungiyoyin nahiyoyin ba Muddin dai suna ɗaukaka da ra'ayi da manufar majalisar ɗunkin duniya. Don haka yana baiwa ƙasashen da ke cikin waɗannan Nahiyoyin domin magance matsalar da ta taso da kuma bunƙasa zaman lafiya a duniya. Kamar dai yadda "Matakan kawo zaman lafiya' ya ambata, waɗannan ƙangiyoyin suna iya ƙunsar ƙungiyoyin sulhu, babu damuwa ƙungiyoyin sun samu n e bayan kafa majalisar ɗunkin duniya ko kafin kafa ta, ko sun samu ne ta hanyar samar da tsaro da zaman lafiya ko domin cigaban Nahiyoyin ne a gefen tattalin arzika.

Kungi-yoyin Nahiyoyi sun fara taka muhimmin rawa tare da hadin gwiwa da majalisar Ɗunkin Ɗuniya. Kungiyoyin sun haɗa da ƙungiyar haɗin kan Afirka da ta walwale matsalar kudancin sahara da laberiya, ko ƙungiyar sulhu ta Arewacin haɗin gwiwar majalisar Ɗunkin Ɗuniya, lura, da hana keta sararin sama a wasu sassan Bosniya.

## 13 Yaya ne kundin tokar ya samar da sha'anin tattalin arziki da cigaban jin daɗin jama'a?

Babi na IX da na X a tsarin mulkin majalisar Ɗunkin Ɗuniya sun yi magana ne a kan niyar da majalisar ta ke da shi ne na bunƙasa hanyar rayarda jama'a, samar da hanyoyin walwale matsalar tattalin arziki da ta jin daɗin jama'a, da mutunta haƙƙin Bil'adama. Babban reshen da aka ƙirƙiro domin kula da yin hakan shi ne majalisar tattalin arziki da jin daɗin jama'a.

Majalisar tattalin arziki da jin daɗin jama'a na iya ƙaddamar da nazari da rahoto a kan tattalin arzikin duniya, jin daɗi, al'adu, ilimi, kiwon lafiya da sauran su sannan kuma su ba da shawarar abin da ya dace abi ga babban taron majalisar Ɗunkin Ɗuniya. Har-ila-yau wannan reshen na iya ba da shawarar hanyar da za'a bunƙasa mutunta haƙƙin Bil'adama da kuma ƙasidu da za'a baiwa Babban taron majalisar Ɗunkin Ɗuniya. Haka wannan reshen na iya shirga taron ƙarawa juna ilimi na duniya kan waɗannan maganganu, sanna su ƙarfafa wa mutane da gwaunatocin ɗaukan matakai akan matsalar da duniya ta ke ciki.

Majalisar tattalin arziki da jin daɗin jama'a na da ikon sanya ido ga aikace-aikacen majalisar Ɗunkin Ɗuniya, wanda ya ƙunshi shirye-shiryen da babban taron majalisar ya ƙirƙiro, kamar Asusun ƙananan yara (UNICEF) da kuma ofishin kula da 'yan gudun hijira, da dai wasu kafafen musamman na majalisar Ɗunkin Ɗuniya kaman su ƙungiyar lafiya ta Ɗuniya ko Kungiyar ƙwadago ta Duniya. Su dai kafafen nan na musamman sune ƙungiyoyi masu zaman kan su da hedikwatarsu da kuma kasafin kuɗinsu da mambabinsu; majalisar tattalin arziki da jin daɗin jama'a na iya ƙulla wasu alƙawurra da su domin samun wata alaƙar musamman da majalisar Ɗunkin Ɗuniya. A yau akwai tsare-tsare da kafefen musamman fiye da guda 30 da suka taru suka ƙunshi kaso da yawa na shirin majalisar Ɗunkin Ɗuniya, kuma sun shafi duk wani fanni na cigaban rayuwar Ɗan'Adam kama daga kasuwanci ya zuwa harkokin da ya shafi sufurin jiragen sama.

A cikin watan mayu 1994, Babban magatakarda ya bayar da rahoto da aka sani da "matakan cigaba da cewa neman cigaba dole ne ya zamo a fannoni iri-iri kuma a yi shi cikin lumana, tattalin arziki, Muhalli hukunci mai adalci da demokura ɗiyya. Wasu muhimman sassa nea ra'ayin ƙasashen da ke cikin ƙungiyar da kuma martanin da Babban magatsakardar ya ba da a matsayin amsa. Babban magatakardar ya yi bayani ƙarara cewa neman cigaba shi ne ƙalubalen da Ɗan'Adam ke fuskanta "amma talalaɓiya na neman ɗaukar mu ta ɓatar da mu wajen gaugawar ganin mun samu zaman lumana" a marmakon fuskantar barazanan sha'anin cigaba.

## 14 Mene ne hangen nesan da tsarin mulkin ke yi akan wuraren da ba su sami mulkin kai ba?

Shi dai babi na XI da XII da na XII duk sun yi magana ne akan matsaloli da dama da suka shafi wuraren da basu sami 'yancin kai ba. Babi na XI ya ƙunshi cikakken bayani ne akan duk abin da ya shafi wuraren da basu cimma cikakken 'yancin kai ba, da ke kira ga ƙasashen da ke mulkin iri waɗannan wurare da basu da 'yancin kai ba su ba da ƙarfi wajen sha'anin siyasa, ilimi da sha'anin cigaban jin da ɗin mutanen waɗannan wuraren.

Mambobin majalisar Ɗunkin Ɗuniya sun amince da cewa ra'ayin mazauna irin waɗannan wurare shi ne, kan gaba sun kuma "dauki alkawalin ne" na ƙoli da zai sa su yi ƙoƙarinsu don "bunƙasa cigaban magauna waɗannan wuraren kula da jin daɗin mazauna irin waɗannan wurare. A ƙarƙashin Ayar doka ta 73 na kundin dokar tsarin mulkin, ƙasashen da ke mulkin irin waɗannan wuraren sun yi alkawarin sadaukar da kai ga dawainiyar wunaren da ba su da mulkin kai, kuma sun amince da zasu riƙa baiwa Babban sakataren majalisar Ɗunkin Ɗuniya bayani akan tattalin arziki, jin daɗin jama'a, ilimi, da cigaban da aka samu a irin wuraren da suke shugabanta.

Tsarin majalisar amintattu an ƙirƙiro shine a ƙarƙashen Babi na XII domin lura da wuraren amana, a inda majalisar Ɗunkin duniya duniya zata kula da sha'- anin mulkin wuraren amanar. Wuraren amana wurare ne da basu sami mulkin kai ba amma masu mulkin waɗannan wuraren suka bayar da su amana ga majalisar Ɗunkin duniya dangane da wani alkawari da suka ƙulla. Majalisar amintattu ta kakkaɓe hannunta ga mulkin ƙasar amana ta ƙarshe watau—Tsibirin palau bayan tsawon kusan rabin ƙarni da ta yi tana mulkin sa, shi dai wannan tsibirin da ƙasar Amurka ce ke mulkin sa kafin majalisar Ɗunkin Ɗuniya ta karɓe shi Yanzu ya sami 'yanci a watan oktoba 1994.

A 1960, Babban Taron Majalisar Ɗunkin Ɗuniya ya amince da baiwa 'yanci ga duk ƙasashen da ke ƙarƙarshin mulkin Mallaka, domin bunƙasa mulkin kai, majalisar amintattu na riƙe ne kawai da wurare II wasu kuma suna baje a duniya. An kafa kwamitin musamman da zai kula da gaggauta samar da mulkin kai ga ƙasashe. A ƙoƙarin da majalisar Ɗunkin duniya ta ke yi a fannin samar da 'yanci ga ƙasashe fiye da wurare 70 ne masu 'jimillan yawan mutane miliyan 750 suka sami 'yanci tuni har sun shiga cikin ƙungiyar majalisar Ɗunkun Ɗuniya.

## 15 Mene ne abin da kundin tsarin Mulki ya ce akan Babban sakatariya?

Kundin tsarin mulki ya ɗauki sakatariya a matsayin babban reshen majalisar ɗunkin duniya (duba tambaya ta 5 a sama). Ayar doka ta 97 ta ce sakatariya zata ƙunshi Babban magatakarda da ma'aikatan da ƙungiyar ke bukata. Ayar doka ta 100 ta yi bayanin cewa ma'aikatan ba zasu karɓi doka daga duk wata gwamnati ba; haka nan babu wata ƙasar da zata yi ƙoƙarfin ta'asiri ga maāikatan yayin da suke gu danar da aikinsu. Amma kundin bai yi magana ba akan yadda za'a tsara sakatariyar ba. Sakatariyar zata ƙunshi ma'aikata 'yan ƙasashe daban-daban ko ma'aikata da zasu yi aiki ƙarƙashin Babban sakataren majalisar Ɗunkin Ɗuniya domin amfanin ƙasashen da ke cikin ƙungiywar. Akwai ma'aikata 29,000 ga sakatariyar majalisar daga sassan daban-daban na duniya. Su kuma kafafen musamman na majalisar na da ma'aikatansu da suka fito a sassa daban-daban na duniya da ya kawo yawan masu yi wa ƙungiyar aiki da suka dara 50,000 yawa da kaɗan.

## 16 Wace ayar doka ce daga cikin kundin tsarin mulkin ya yi magana akan aikin Babban Magatakardar ƙungiyar?

A yar doka ta 97 ta yi bayani cewa Babban sakataren ƙungiyar shi ne babban mai gudanar da sha'anin mulkin sakatariyar ƙungiyar.

A yar doka ta 98 ta umurci Babban magatakardar majalisar ne da ya riƙa baiwa majalisar rahoto shekara-shekara akan aikace-aikacen ƙungiyar. Wannan rahoton na shekara-shekara ba wai kawi zai baiwa Babban sakataren daman jawo hankalin ƙungiyar ba ne kan abubuwan da ke gabanta a'a yana ƙara fahimtar da ita muhimman matakan da ya kamata ta ɗauka.

A yar doka ta 99 kuma tana baiwa Babban magatakardar ƙungiyar dama ce da ya kai bayanin duk abin da ya ke hangen zai zama barazana ga sha'anin tsaro da zaman lumana a duniya ga majalisar tsaro. Misali lokacin da yaƙin kongo ya ɓarke a 1960, Babban sakataren wannan lokacin Dag Hammarsjold ya kai maganar agaban majalisar tsaro, ta yin amfani da karfin da doka ta bashi ƙarƙashin ayar doka ta 99 tun farkon kama mulkinsa. Ayar doka ta 99 da aka yi amfani da ita a baya-bayanrnan shi ne a 1989 a maganar ƙasar lebanon da. Babban sakataren wannan lokacin Javier perez de cuellar ya yi.

## 17 Wace hanya ce kundin tsarin mulki ya ce a tsara kasafin kuɗin majalisar Ɗunkin Ɗuniya?

Idan aka yi la'akari da ayar doka ta 17 ta tsarin mulki, Babban taron majalisar shi ke da haƙƙin lura da amincewa da kasafin kuɗin. Su kuma kasashen da ke cikin ƙungiyar ke da haƙƙin samar da kuɗin da majalisar zata aiwatar da aikace aikacenta daidai da irin kason da Babban sakatare ya tsaga wa kowace ƙasa.

Kwamitin tarbace (ga ƙasashe), wanda ya ke wani yanki ne na Babban taron majalisar shi ke da haƙƙin shata hanyar da ƙasashe zasu san irin kason da zasu bayar. Mambobin ƙungiyar za'a yi nazarin karfin tattalin arzikinsu da yawan kuɗin shigarsu da yawan mutanensu; sannan a faɗi abin da ake ganin ƙasa zata iya biya. Dangane da hukuncin da Babban taron majalisar ja yanke a 1972 mafi yawan abin da ƙasa za'a amince ta biya daga kasarƙarancinfin ƙungiyar na she kara shi ne kashi 25 cikin ɗari, haka mafi a bin da za a biya shi ne 0.01a cikin ɗari.

## 18 Idan ƙasashe suka ƙi mutunta tanaje-tanajen da tsarin mulki ya yi, mene ne za'a yi akan haka?

Yayin da ƙasashe suka bijire wa abin da tsarin mulki ya yi tanadi, ko hukuncin wani reshe daga cikin manyan ressan ƙungiyar da majalisar Ɗunkin Ɗuniya ta kira da a mutunta, Kungiyar na iya ɗaukan matakai daban-daban, koda yake ya dogara daga irin zurfin keta alfarmar dokar da aka yi. Kasashen da suka ki biyan kasonsu na kasafin kuɗin majalisar har ya kai yawan abin da aka tsaga wa kasar har na shekaru biyu zasu fuskanci hukuncin hana su yin zaɓe a cikin Babban taron majalisar, amma idan har dalilin da ya hana kasar biyan kasonta mai ƙarfi ne (misali Kamar wata masifar da ta faɗa masu) ana yi ɗage takunkumin yin ƙuri'ar gareta. Har-ila-yau dai mun san wannan doka ba'a taba tsaurara ta ba.

Yayin da kasashe suka keta alfarmar zaman lumana ko kai ma wata ƙasa hari ko ƙin bin hukuncin da majalisar tsaro ta yanke kan abin da yake barazana ga zaman lafiya a duniya, ana iya ɗaukan matakan ganin an bi wannan hukuncin kamar yadda Babi VII na kundin tsarin mulki ya ce (duba tambaya ta 9).

Yayin da ƙasashe suka keta haƙƙin Bil'adama, Majalisar da ke kula da haƙƙin Bil'adama wanda ya ke wani ɓangare ne na majalisar tattalin arziki da jin daɗin jama'a zata tattauna akan tsananin keta haƙƙin Bil'adaman da aka yi. Kwamitin kula da haƙƙin Bil'adama—Wanda aka ƙirƙiro domin ya sanya Ido akan dokar da aka yi ta duniya kan haƙƙin Bil'adama, dokar 1966 ta duniya da aka yi akan haƙƙokin fararen hula da haƙƙin siyasa-na iya bincikawa domin ganin ko da ƙasashe na bin wannan dokar. Majalisar tsaro a 1993 ta kafa Wata kotun tafi-da-gidanka domin gurfanar da murtanen da ke da laifukan yaƙi a tsohuwar ƙasar Yugoslbiya (duba tambaya ta 9).

Saɓannin abin da mutane suka yi imani da shi cewa ba'a

iya kawo ƙaran ƙasashe gaban katun duniya domin rashin bin wata doka ta tsarin mulkin majalisar Ɗunkin Ɗuniya. Ana iya kawo ƙaran wani saɓani da ke tsakanin ƙasashe a gaban kotun duniya, kafan musamman na iya newan shawarar kotun ko kuma wani reshen majalisar Ɗunkin Ɗuniya da ya dace da ya yi haka. Kotun ta ƙunshi alkalai goma sha biyar da za'a zaɓa har tsawon shekaru tara-tara.

Karfin siyasa da kyakkyawar imanin da ƙasashe suke da shi, shi ne majalisar ta dogara da shi domin samun nasarar ayyukanta. Ayar doka ta 5 na tsarin mulkin majalisar Ɗunkin Ɗuniya ya yi tanadin dakatar da duk wasu haƙƙoƙin ƙasa na matsayinta na mambar-ƙungiyar tsaro ta sanya mata matakan hana ta ko na ƙarfata mata yin abin da ta kasa yi. Mataki da ke gaban wannan shi ne kora baki ɗaya daga cikin ƙungiyar wanda zai hana wasu ƙasashe su daina irin wannan laifin. Gaskiyar lamarin dai shi ne ƙasashen da ke cikin wannan ƙungiyar na gaskata cewa suna cikin al'umar Duniya, don haka dole ne a yi masu hukunci akan irin abin da suka aikata, kuma dole ne su aiwatar da abin da ya ke ɗawainiyarsu ce.

## 19 Tsarin mulkin majalisar Ɗunkin Ɗuniya ya yarda da ƙasa ta fita daga ƙungiyar ko kuma a kore ta?

Ayar doka ta 6 ta ce wata ƙasar da ke cikin ƙungiyar Ɗunkin Ɗuniya da ta yi ta keta manufofin da tsarin mulkin majalisar ya ƙunsa Babban taron majalisar ƙungiyar na iya korar ƙasar daga cikin ƙungiyar da amincewar majalisar tsaro . Har yanzu dai ba'a kai ga taba korar wata ƙasa daga cikin ƙungiyar ba. Duk da haka dai akwai ƙasashen da aka mayar saniyar ware akan aikace aikacen Babban taron majalisar, kamar Afirka ta kudu tsakanin 1974 da 1994 da tarayyar Yugoslabiya (sabiya da monteniguro) tun 1992. Kowane lokaci Babban taron majalisar ya ga dama na iya soke wannan hukuncin.

Tsarin mulkin bai yi tanadin cewa wata ƙasa na iya fita daga ƙungiyar ba. Kasar indonesiya ta fice daga ƙungiyar ta dawo shekara mai zuwa.

## 20 Ana iya yi wa tsarin mulkin gyaran fuska kuma hakan ya taba faruwa?

20. Ayar daka ta 108 ta ce ana iya yi wa tsarin mulkin kwas kwarima. Kafin a yi gyaran dole ne sai an sami ƙuri'ar kashi biyu cikin uku na Babban taron majalisar da suka amince da yin hakan. Rinjayen kashi biyu cikin ukun zai haɗa da ƙasashe masu kujerin dindindin daga cikin majalisar tsaro, sannan sai a ɗauki matakan yin gyaran ga tsarin mulki dai-dai da yadda doka ta ce.

An yi wa tsarin mulkin kwaskwarima sau uku, domin ƙara yawan majalisar tsaro a (1965) da lokacin da aka ƙara yawan majalisar tattalin arziki da jin da ɗin jama'a a (1968, 1973).

## 21 Wasu matakai ke tafe da zai sa a yi nazarin tanaje-tanajen tsarin mulkin?

## An taba yin tattauna wa akan yadda za' a canza o mambobin majalisar tsaro da yadda suke jefa ƙuri'a?

Kasashen da ke cikin ƙungiyar Ɗunkin Ɗuniya na nan na nazarin muhimmanci da dacewar Kundin tsarin mulkin ƙungiyar ga rayuwar duniya ta yau da ta samu wani sauyi mai ban mamaki tun lokacin da aka kafa ƙungiyar majalisar Ɗunkin Ɗuniya. Cikin 'yan shekarun nan wani ƙaramin kwamitin Babban taron majalisar da ake kira kwamitin musamman akan tsarin mulkin majalisar Ɗunkin Ɗuniya da ƙarfafa rawar da ya ke taka wa shi ne ke gudawar da alkace aikacen nazarin tsarin mulkin majalisar, domin ganin sashen da ya dace da gyara.

A 1992, Babban taron majalisar ya tattauna akan yadda aka tsara majalisar tsaro. Majalisar ta amince da irin canjin da duniya ta samu don haka Babban taron ya kira ga a faɗaɗa yawan majalisar tsaro. Babban taron ya amince da a isar wa Babban magatakardar kungiyar saƙonsa na musamman akan tsarin mulki da ya shafi faɗaɗa yawan majalisar tsaro da yadda za'a sami wakilai cikin ƙungiyar a kowace nahiyoyin duniya yawan su ya zame ɗaya. 'Yan ƙungiyar na so ne a faɗaɗa yawan mambobi masu kujerin dindindinda waɗanda basu da kujerun dindindin na majalisar tsaron, da kujerun na-ƙi ko waɗanda basu da kujerun na-ƙi ga ƙasashe na daban bayan ƙasashe biyar ɗin nan masu kujerun dindindin, wa ɗanda a halin yanzu ke da damar hawan kujerar na-ƙi. Har-ila-yau suna da ra'ayin ganin an sami kwaskwarima a wasu fannoni na sha'anin majalisar tsaro, kamar hanyar da ake jefa ƙuri'a adalcin majalisar wajen hukanci da alakar majalisar da wasu rassan majalisar Ɗunkin Ɗuniyar, musamman ace alaƙarsu da Babban taron majalisar. A 1993 Babban taron majalisar ya amince da kafa wani kwamiti da zai yi aiki domin faɗaɗa majalisar tsaro inda za'a yi rabon da ya ke na adalci ne ga duk nahiyoyin duniya.

## 22 Ko tsarin mulkin ƙungiyar majalisar Ɗunkin Ɗuniya ya kasance ya dace da shekarun da ake yanzu?

An sha yin bayanin cewa an tsara tsarin mulkin ne sanadiyyar abin da ya jawo yaƙin Duniya na biyu, don haka bai dace ba da halayyar da duniya take ciki a yau ba da irin yaƙe-yaken da ake yi a cikin ƙarshen ƙarni na ashirin. Duk da haka dai mambobi sun haƙiƙance cewa tsarin mulkin abu ne da za'a iya fassara shi ta yadda zai iya dacewa da duk irin yanayin da aka samu kai da irin cigaban da ake hange. Ba shakka gyaran fuska ga tsarin mulkin abu ne mai muhimmanci don haka nan gaba za'a iya yin hakan. TSarin mulkin yayi juriyan yin aiki na rabin ƙarni, da hikimar 'yan ƙungiyar tsarin mulkin na iya samar da abin da ake bukata a gare shi. Tsarin mulkin a dunƙale ya ke ba awalwale shi ba. Saboda sauƙin fasararsa da hangen nesan da yake ɗauke da shi shi ya sa yake da inganci mai yawa.

## An shawarce ka ka karanta wadannan.

Tsarin mulkin majalisar Ɗunkin Ɗuniya (na sayarwa ne)

- Matakan samar da zaman lafiya mai sabon mujalladi (na sayarwa ne)
- Matakan cigaba (na sayarwa)
- Majalisar Ɗunkin Ɗuniya a Dunkule
- Sura da gaskiyar al'amari
- Gaskiya akan majalisar Ɗunkin Ɗuniya (na sayarwa)

Don ƙarin bayani sai a tuntuɓi cibiyar watsa labarai game da majalisar Ɗunikin Ɗuniya da ke kusa da kai, ko sashen da jama'a ke yin bincike akan majalisar da ke ɗaki GA – 57 Majalisar Ɗunkin Ɗuniya a Birnin New York, NY 10017

Kasidun sayarwa kuwa sai a tuntuɓi Ɗakin wallafe-wallafe na majalisar Ɗunkin Ɗuniya mai lamba DC2–853 New York, NY 10017 Ko Ɗakin sayen wallafe–wallafen majalisar Ɗunkin Ɗuniya da Ɗakin karatu CH–1211 Geneva 10,
Kasar Switzerland.

Published by the United Nations Information Centre
17, Kingsway Road, Ikoyi, Lagos, Nigeria.
DPI/1738-13403-November 2000